



Malam Garba na da 'ya'ya uku.
Sani da Sambo da Ladidi sune yaran.
Malam Garba ɗan kasuwa ne.

Duk yaran Malam Garba
suna makaranta.
Sambo ya cika kwaɗayi.
Ladidi tana da basira.
Ba ta son rashin gaskiya.



Wata rana kuɗi ya ɓata.
Malam Garba ya kira
'ya'yansa.
Ya tambaye su wanda ya
ɗauki kuɗi.
Kowa ya yi shiru.




A makaranta Ladidi ta lura.
Sambo na sayan kayan kwaɗayi.
Ladidi ta sanar da babansu.



Babansu ya sake tara su.
Ya fara neman kuɗinsa.



Ya duba jakar Sani ba kuɗi.
Ya duba jakar Ladidi ba kuɗi.
Da ya duba jakar Sambo sai ga kuɗi.
Malam Garba ya fusata.





Sambo ya amsa laifinsa.
Ya kuma tuba.
Aka yafe masa.



Sambo ya zama yaron ƙwarai.